# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yoshuwa ya Dauki Shugabanci




Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Janie Forest
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen



Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org



©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.




Musa ya mutu. Yoshuwa ya sani cewa Allah ya zabe shi ya shugabanci Isra'ilawa. Kafin Yoshuwa ya shirya sojojinsa, dole sai ya shirya kansa. Allah ya yi wa Yoshuwa alkawrin nasara da ci gaba a kasar Alkawarin idan mutanen za su yi biyayya ga Kalmar Allah kullum.



Isra’ilawa suka yi alkawari za su bi Yoshuwa su kuma yi biyayya ga Kalmar Allah kullum.



Cikin hikima, sabon shugaban ya aike ‘yan leken atsirin kasa zuwa Kan’ana domin bincike irin tsaron da kasar take da shi na wannan babban birnin Yeriko. A wurin ne farkon yaki na Isra’ila zai kasance.

3



Wani ya gaya wa Sarkin Yeriko cewa akwai ‘yan leken atsirin kasa a gari. Sai ya aike sojoji a neme su. Binciken ya fara a gidan Rahab, inda mazan suke zama. Sojojin sun kwankwasa da karfi a bakin kofar. Da sauri-sauri, Rahab ta boye mazan a karkashin wani wuri.

4

Bayan da sojojin suka tafi, Rahab ta yi amfani da wani gyale domin ta saukar da su zuwa kasa a bangon birnin. Don me ta taimake ‘yan leken atsirin? Saboda ta sani Allah yana tare da su. Tana so Allah ya cece ranta. ‘Yan leken atsirin suka yi alkawari za su cece ta da iyalinta.



5

Kafin su kai Yeriko, dole sai Isra’ilawa sun ketare Kogin Yodan zuwa Kan’ana, Kasar Alkawari. Amma babu gada! Yaya ne mutanen za su ketare?



6

Allah ya gaya wa Yoshuwa cewa firistoci za su jagorance sojojin da mutanen, suna dauke da Akwatin wanda yana kunshe da Dokoki Goma. Sa’ad da tafin kafan firistocin ya taba bakin kogin, Allah ya yi abin ala’ajibi. Allah ya bude bushashiyar hanya a tsakiyar ruwan.



7

Bayan da duka mutanen suka ketare lafiya lau, sai suka kafa manyan duwatsu guda goma sha biyu a gindin kogin, guda gomma sha biyu kuma a bakin kogin Kan’ana. Wadannan sun zama abin tuni domin taimaka wa mutanen yadda za su koyar wa ‘ya’yansu game da babban iko da kaunar Allah.



8



Yeriko yana da katanga mai karfi da kauri kuma. Sa'ad da Yoshuwa yana shirin kai wa garin hari, Allah ya aika da Shugaban sojojin Sa daga Sama domin ya tunashe sabon shugaba na Isra'ila cewa Allah ne yake cin nasara a yaki wa mutanen Sa.

9



Allah ya gaya wa Yoshuwa yadda zai kai wa Yeriko hari. Wani shiri ne wanda ba a saba da shi ba. Mutanen Allah za su kewaye birnin kowace rana sau daya har na kwana shida. A rana ta bakwai za su kewaye birnin sau bakwai. Sa'an nan za su huraa kaho suna ihu, sai bangon birnin zai rushe ya fadi kasa gaba ki daya.

10

Yoshuwa da sojojinsa suka yi daidai yadda Allah ya umarta. Watakila mutanen Yeriko sun yi musu dariya. Amma, bayan kewayewa ta bakwai a rana ta bakwai firistoci suka huraa kahonin raguna. Daidai kamar yadda Allah ya yi musu alkawari… BABBAN KATANGAN YERIKO YA RUSHE.









11



Gidan Rahab ne kadai wanda ya tsira daga rushewar bangon. Ta bar dankwalinta yana lillo daga tagan gidanta. Nan da nan mutanen Yoshuwa suka kubutar da ita da iyalinta. Sai aka halakar da birnin Yeriko kamar yadda Allah ya umarta.

12



Cikin ibada, Yoshuwa ya mika zinariya, da azurfa, da kayan arziki na Yeriko domin a yi wa Allah hidima. Sa'an nan ya sa la'ana a kan duk wani wanda zai sake gina wannan mugun birnin. Ba a dadde ba sai kowa a Kan'ana ya ji labari yadda Yoshuwa ya ci nasara a kan Yeriko. Suka sani cewa Allah yana tare da mutanensa.

13

Yoshuwa ya Dauki Shugabanci

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Yoshua 1-6

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

14




13

60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**